




Biri na da wayo.


Akuya kuma wawiya.



Biri da akuya suna


noma.

Suna noma tare.



Sun shuka dawa.

Dawa ta yi kyau.



Sun yanke dawa.

Ina za su ajiye dawa?




Biri ya ce kan bishiya.

Akuya ta amince.




Biri ya hau bishiya.

Dawa na kan bishiya.



Akuya na son dawa.

Biri ya ce ta hau.



Akuya za ta hau

bishiya?

Akuya wawiya ce.